# Yaki da murzuna ba tare da zuba maganin miyagun kwari , abune ne mai yiwa !

*Madougou Garba (DGPV), Haougui Adamou et Bibata Ali (INRAN), Aïssa Kimba et Patrick Delmas (RECA), Boukari Harouna (Union Haraybane Téra Mooriben) / 13 Mai 2018.*



Manoman kasar Nijar na cigaba da fuskantar barazar muguwar tsutsar nan mai cinye kwayar gero wanda ake cema MURZUNA.

MURZUNA na apkama hatsi ne a lokacin da ya fidda kaye kuma manomi ke zaton cewa zai samun samu hatsi sosai ; nan da nan sai ta cinye kwayar geron idan ba'a dauki mataki ba da wuri sai ma ta ciye hasti ga baki daya.

Lokacin da murzuna ta bayana a cikin wani yanki ta kan iya mamaye ilahirin gonankan dake wajan sanan kuma magani baya tasiri a kanta.

Aman akoye wata hanyar yaki da wanan tsutsar MURZUNA.

Zamu gabatar muku da husa'ar nan ta renon diyan rina wanda turawa ke cema HABROBRACON.



Rina wani dan karamin zanzaro ne mai kama da zuma kuma ya shahara wajan yaki da MURZUNA saboda diyan ta ke cinye tsutsar.

Karamcin rinar da ake fama dashi baya iya kashe tsutsar,gata kuma da yawan aihuwa.

Saboda haka dole sai manoma sun dage wajan kiwon rinar dan tayi yawa suji dadin yaki da stustar (MURZUNA).

Wasu kungiyoyin manoma na TERA da DANTCHANDU a cikin jahar Tillaberi sun kware wajan kiwon na rinar.

Wanan kungiyoyin manoman sun samu horo ne na musaman kuma suna cigaba da sayar ma wasu manoma dan su rinka kare gonankansu; wanan husa'ar ta kungiyar manoma HAREYBANE ta Tera, daya daga cikin menbobin babbar kungiyar MOORIBEN ce zamu bayana muku a yau.

## Mi cece tsutsar hatsi murzuna ?



Malan batatan dake haihuwar tsutsar ta hatsi na bayana ne wata guda bayan ruwa fari wato ruwan da zai ba manoma dammar yin shipka.

Maccen malan batatan na zuba kwayayanta ne bisa zangarniyyar hasti da ya fara hure.

Bayan kwanaki 3 zuwa 4,kwayayan nan sai su kinkeshe sai wata tsutsa ta bayana ta rinka cinye hastin tsawon wata guda.

Bayan wanan sai ta fadin kasa ta niste cikin kasa tsawon watanni tana jiran wata damina ta dawo ta rikide ta koma wani sabon malan batata kuma ta sake wata sabuwar banna.

## Mi cece rina ?



Rina dai wani dan karamin zanzaro ne mai kama da zuma.

Maccen rina na zuba kwayakonta ne saman tsutsar,da sun kinkashe sai diyan zanzaro nan su rinka cin kaskon murzuna nan kamar yadda kuke gani a jikin wanan hoton.

Kungiyar Harey bane ta Tera ta kware wajan renon rinar, ta saka ta cikin buhuwa kuma ta sayar ma manoma dake unfani da ita wajan kare gonankan su.

## Yaya ne suke yi ?

Da farko dai ya kamata manoma sun san lokacin da ya dace domin sun shirya rinar daidai lokacin da hatsi ke shirin fara fure kenan a watanin Juillet ko Aout.

Kahin wanan lokacin murzuna bata fara ba ,kenan sai an samo wata tsutsar wato diyan karamin malan batata mai sunan Corcyra wanda ake iya samu cikin maganza na ajiyar abinci sanan a fara renon diyan rinar.

Masu renon zasu debo malan batatan dake haihuwar COrcYRA a farkon watan Mayu sai su saka su cikin wasu bokiti su zuba hasti.

A saman tsutsar Corcyra ne renon zanzaron zai fara

## Da wane lokaci ne ya kamata a fara renon rinar ?

A cikin watannin juin da juillet kuskudun tsutsar dake rikidewa ya koma diyan rina za'a zuba cikin bokiti bayan kwanaki kadan sai su rinka zuba kwayakoye;

Daga bisani kuma sai, a samu yan kananan kumusa masu centimeter 10 wanda za'a saki cikin gona,a cikin su akoye hasti kadan,macen rina biyu masu kwai da tsutsar Corcyra 25.

Bayan kwanaki 8 da shirya kumusan,za'a iya samun diya rina 50 zuwa 70 a tsawon sati biyu.

Renon rinar abu ne mai wahala,saida kwararan sani da kuma ilimi kenan sai an samu horo sosai kuma da hakuri.

## Yaya ake sakin rinar ?



Ana saka guda 15 a cikin kowane bangare na gona da kuma tsakiyar karkara.

Wanan kumusan 15 sun isa su kare gonankan karkara a cikin kewayen kilo meter 5 daga jikin gari.

Ana saka yan buhunan ne kalkahin wani yankin bunburutu na ruwa ko kuma wata kwarya don kare su daga iska ko ruwa.

Daga bisani sai zanzaron su rinka hutowa suna cinye murzuna dake saman geron.

## A nawa ne mazamnan wani kauye ke iya samun kumunsan na diyan rina?

Kungiyar Harey bane ta Tera na sayarda buhu guda a jika 2.

In kauyen na bukatar yan buhuna 15 to zai tasan musu a jika30 kenan in yawan manoman ya kai mutun 100, to ko wane manomi zai bada dala 300.

In kuma yawan gidajan ya kai 300 to kowane magidanci zai bada dala 100 don kare gonar shi.

Kenan a game da gona mai fadin eka guda, ko, manomi bai kashe kudi ba zai sayi magani na jika 4 duk da rishin tabacin cewa zai samu nasarar kashemurzuna.



Ya kamata manoma su sanar da kungiyar ta Harey bane tunda wuri don su samu damar shirya musu adadin buhunan da suke bukata saboda renon rina da shirya buhuhuwa abu ne mai wahala da kuma daukan lokaci;

Saboda haka kuyi kokarin kiran kungiyar a kan wanan lambobin 96 47 00 75.

Wasu kungiyoyin manoma na reno kuma suna sayar da buhuwan rina;wanan kungiyoyin sune na Dantchandu a cikin jahar Tillabery da kungiyoyin manoma na Sae Saboua, Guidan Sori, Sarkin Haousa ko Sarkin Bindiga a cikin jahar Maradi.

Idan kuna bukatar Karin bayani to sai ku tuntubi mashawartan nan na kugiyoyin **RECA** da **CRA** kan **92 24 24 24** (Orange) ; **89 97 97 74** (Airtel) ; **84 74 74 74** (Moov) ; **93 32 38 92** (Niger-Telecoms) ko kuma WhatsApp a kan **92 24 24 24.**

Wanan layoyin dai kungiyoyin **RECA** da **CRA** ne suka tanadar muku su don waye muku kai kan ayyukan ku na noman gandari.

---

Cette note correspond au contenu d'une émission radio diffusée dans les différentes régions et dans les différentes langues du Niger. Le contenu de l'émission a été préparé par des techniciens du Réseau National des Chambres d'Agriculture (RECA) et des producteurs de l'Union Haraybane, de l'Institut National de la Recherche Agronomique et de la Direction Générale de la Protection des Végétaux avec les appuis financiers du **Projet d'Appui à l'Agriculture Sensible aux Risques Climatiques (PASEC)** et du **Programme de Productivité Agricole en Afrique de l'Ouest (PPAAO)**.